# GOD'S SIMPLE PLAN OF SALVATION FROM LUKE

## 1. We are all sinners!

Luke 5:31-32  Yesu ya amsa musu ya ce, "Ai, lafiyayyu ba ruwansu da magani, sai dai marasa lafiya. Ba domin in kira masu adalci na zo ba, sai dai masu zunubi, su tuba."

Luke 18:19  Sai Yesu ya ce masa, "Don me ka kira ni managarci? Ai, ba wani Managarci, sai Allah kaɗai.



**We are all sinners!**

## 2. There is a price for that sin!

Luke 16:15  Sai ya ce musu, "Ku ne masu baratar da kanku a gaban mutane. Amma Allah ya san zukatanku. Abin da mutane suke girmamawa ƙwarai, ai, abin ƙyama ne a gun Allah.

Luke 9:5-6   Duk waɗanda ba su yi na'am da ku ba, in za ku bar garin, sai ku karkaɗe ƙurar ƙafafunku don shaida a kansu."   Sai suka tashi suka zazzaga ƙauyuka suna yin bishara, suna warkarwa a ko'ina.

## 3. Jesus died and paid for our sins on the cross!

Luke 18:13  Mai karɓar haraji kuwa yana tsaye daga can nesa, bai yarda ya ɗaga kai sama ba, sai dai yana bugun ƙirjinsa, yana cewa, 'Ya Allah, ka yi mini jinƙai, ni mai zunubi!'

Luke 19:10  Don Ɗan Mutum ya zo ne musamman garin neman abin da ya ɓata, yǎ cece shi kuma."

Luke 24:46  ya kuma ce musu, "Haka yake a rubuce, cewa wajibi ne Almasihu ya sha wuya, a rana ta uku kuma ya tashi daga matattu,



**Christ died for sinners!**

# 4. Salvation is a free gift, not by good works. You must take God's word for it, and trust Jesus alone!

Acts 4:12 Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyar nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto."

Eph 2: 8-9 Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda da aikin lada ba, kada wani ya yi fariya.

Tite 3:5sai ya cece mu, ba don wani aikin adalci da mu muka yi ba, a'a, sai dai domin jinƙan nan nasa, albarkacin wankan nan na sāke haihuwa, da kuma sabuntawar nan ta Ruhu Mai Tsarki,

# 5. You must put your faith and trust in Christ alone.

Luke 13:3 Ina gaya muku ba haka ba ne! In kuwa ba ku tuba ba, duk za ku hallaka kamarsu.

Luke 18:17 Hakika, ina gaya muku, duk wanda bai yi na'am da Mulkin Allah kamar yadda ƙaramin yaro yake yi ba, ba zai shiga Mulkin ba har abada."

Romans 10:9-10,13 Wato, in kai da bakinka ka bayyana yarda, cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. Domin da zuci mutum yake gaskatawa yǎ sami adalcin Allah, da baki yake shaidawa ya sami ceto. "Duk wanda kuwa ya yi addu'a da sunan Ubangiji zai sami ceto."



**Put your faith and trust in Christ alone!**

*Idan kana son ka karɓi Yesu Kiristi a matsayin mai cetonka, ga samfurin addu'a anan. Ka tuna, faɗar wace nan addu'a ko wata addu'a dabam ba zai cece ka ba. Amincewa ce kaɗai cikin Kiristi wanda zai iya cece ka daga zunubi. Wace nan addu'a, hanya ce mai sauƙi a furta ga Allah bangaskiyarka a cikin Sa kuma ka gode masa don ya tanadar maka da ceto.*

**"Allah,**

**na sani cewa nayi zunubi gareka kuma na cancanci hukunci. Amma Yesu Kiristi ya ɗauki hukuncin da ya cancance ni, don ta wurin bangaskiya a cikinsa in sami gafartawa. Na juyo daga zunubaina kuma na sa amincewa tawa a cikinka don ceto. Na gode maka don alherinka mai ban mamaki da kuma gafara – kyautar rai madawwami! Amin!"**

Amazing Grace Publishing *100 Lakeview Court * Joshua TX 76058 * 817-426-1828 * E-Mail JamesAV@aol.com